# IMAMALINEHANYARALLAH MADAIDAICIY

**Wallafar**

**SheikhDhiya'ulJawahiri**

**Fassarar**

**Mal.MunirMuammadSa'id**

**Da**

**MAL.NasiruIsa**

WWW.KETAB.IR

نام کتاب: علي صراط الله المستقيم
تأليف: الشيخ ضياء الجواهري
مترجم: منير محمد و ناصر عيسى
زبان ترجمه: هوسا

علي صراط الله المستقيم هوسا

**Sunan littafi:** Imam Ali ne Hanyar Allah Madaidaiciya
**Mawallafi:** Sheikh Dhiya'ul Jawahiri
**Fassarar:** Munir Muammad Sa'id Da Nasiru Isa
**Bugu:** Na Farko
**Mabuga:** Mihir- Birnin Kum
**Adadi :** **2000**
Farashi:

MU'ASSARA IMAM ALI (A.S)
BIRNIN KUM – IRAN
P.O.BOX: 737/37185
LAMBAR TARHO: +98 25 37743996
LAMBAR FAX: +98 25 37743199
http://www.rafad.net
E-mail: imamali@rafad.net


WWW.KETAB.IR

سرشناسه: الجواهري، الشيخ ضياء
عنوان و نام پديدآور: علي صراط اللّه المستقيم / المؤلف الشيخ ضياء الجواهري
مشخصات نشر: قم، ۲۰۱۸م = ۱۳۹۷ش
مشخصات ظاهری: ۳۴۳ صفحه
شابک: ۲ ـ ۵۹ ـ ۷۱۰۰ ـ ۶۰۰ ـ ۹۷۸
وضعیت فهرست نویسی: فیپا.
یادداشت: هوسایی
موضوع: شیعه ـ تاریخ
موضوع: شیعه ـ عقاید
موضوع: شیعه ـ دفاع ها و ردیه ها
رده بندی کنگره: ۱۳۹۷ ع ۸ ج ۹ / BP۳۷/۳۵
رده بندی دیویی: ۲۹۷/۹۵۱
شماره کتابشناسی ملی: ۵۰۸۳۷۴۴

WWW.KETAB.IR

**هوية الكتاب**

اسم الكتاب ـ علي صراط الله المستقيم
المؤلف ـ الشيخ ضياء الجواهري
الناشر ـ مؤسسة الامام علي عليه السلام
الهاتف / 37743996 25 98+
المطبعة ـ الوفاء
تاريخ الطبع ـ ۲۰۱۸ م ـ ۱۳۹۷ ش
الطبعة ـ الاولى
عدد النسخ ۲۰۰۰ نسخة
ردمك: ۲ ـ ۵۹ ـ ۷۱۰۰ ـ ۶۰۰ ـ ۹۷۸ / ISBN: 978-600-7100-59-2



Da Sunan Allah Mai Rahama Mai
Jin Kai
Tsira Da Amincin Allah Su Kara
Tabbabta Bisa Fiyayyen Halitta
Manzon Rahama Annabi
Muhammad Da Alayensa Tsarkaka

WWW.KETAB.IR

## GABATARWA

Da Sunan Allah Mai Rahama Mai Jin Kai

Manzon Allah (s.a.w) ya ce: "Ni da Aliyyu daga haske ɗaya muke"[1]. Manzon Allah (s.a.w) ya ce: "An halicce ni ni da Aliyyu daga haske ɗaya"[2] Shablanji ya ce: Aliyyu bn Abi Ɗalib (a.s) ya taho, sai Manzon Allah (s.a.w) ya ce: Madalla da ɗan uwana ɗan Baffana ni da shi an halicce mu daga haske ɗaya"[3].

A ranakun haihuwar ɗan Ka'aba shugabana majiɓincina Amirul muminin Aliyyu bin Abi Ɗalib (a.s) a watan Rajab na shekara 42 Hijriyya, na yi nufin kai ziyara makwancin shugabata Faɗima 'yar Imam Musa ɗan Ja'afar (a.s) wacce aka fi sani da Ma'asuma a birnin Kum mai tsarki, bayan nan ne na ta fi Mu'assar Imam Ali (a.s) a wannan birnin da nufin zuwa wajen Hujjatul Islam wal muslimina sheikh Diya'ul Jawahiri ɗan Ayatulllah Muhammad Hasan (ƙ.s) don bijiro da littafi na kan haɗin kan musulunci a bugo na ƙarshe don fassara shi da yaren Duniya da aka fi amfani da shi sai ya karɓe shi, bayan nan sai malamin ya so in ɗan rubuta masa gabatarwar littafinsa (da ya rubuta) mai ƙayatarwa wanda ya ƙunshi taken "Sayyidi Ali ne hanyar Allah Madaidaiciya". Tun a baya da ma malamin ya rubuta littafi kan shugabarmu Faɗimatuz Zahara (as). Sai na ga ya dace gabatarwar littafin ta zama tambayoyin da na taɓa aika wa Babban malamanin nan Ustaz Yahaya Al'alawi wanda ke wakiltar Yaman a ofishin haɗa kan mutanen Afrika da na Asiya, ya kuma amsa su tun a wancen lokacin da na ke zaune a Al-ƙahira, mai karatu ga gundarin abin da wasiƙar ta ƙunsa na tambayoyi da amsoshi kan Imam Amirul muminin Ali (a.s).

---

[1] Manaƙibu sayyidaina Ali (as) shafi 27 bugun Hiadar Abad / Hind.
[2] Masdarin da ya gabata
[3] Yanbi'ul muwadda na ƙanduzi bahanafe shafi 11 /bugun istambul .



WWW.KETAB.IR

# BISMILLAHIR RAHAMANIR RAHIM

Babban malami mai falala ɗan uwana a addini Sayyid Murtadar Ridhawi Allah ya jiɓince shi tare da ni.
Amincin Allah ya tabbata a gare ku tare da wanda ke ɗebe kewa da ku yake kuma natsuwa da abin da kuke kira zuwa gare shi na haɗuwar shi'a da sunna a kan tushen 'yan'uwantaka da soyayya da ƙauna abubuwan da ke jawo rarraba da rabuwar kawuna. Bayan haka ina gode wa Allah da ba abin bautawa sai shi, kuma ina mai gabatar muku da martinina a taƙaice da kuma zaɓo mas'alolin da kuka kawo mini ranar da kuka kawo mini ziyara tare da abokinku Uztaz Wadi'i, wanda bai gushe ba duk da tsufan da ya yi yana nishaɗi a cikin kakar Ustaz Ahmad Rabi'i Almisri. Na yi nufin bayyana abubuwa a fili a cikin abin da na rubuta, Ina neman gafarar Ubangiji kan duk wata zamiya kuma gare shi na dogara wassalam.

Ɗan uwanku: -
Abdullahi Yahayal Al'alawi

WWW.KETAB.IR